Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Human Being Is an Incurable Disease." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/paden-047-mutum-cuta-ne-marar-magani/.

# Mutum Cuta Ne Marar Magani: Ba a Gwaninta Gareshi

[Title and Cover Page]

Fa qāla al-Shāfiʿī Raḍiya l-Lāhu ʿanhu:

Al-nāsu daʾun dafīnun lā dawaʾa lahum

Tahayyar ʿAqlu minhum wa huwa mundhahilun

In kunta munbasiṭan sammūka musharatan

Aw kunta munqabiṭan qālū lahu athaqalu

Wa intakhālaṭahum qālū bihi ṭamaʿu

Aw in tajānabahum qālū abihi al-malalu?

Wa in taʿffafat ʿan amwālihim karaman

Qālū ghaniyyun wa in tasālahum bakhilū

Inni taḥayyartu fī amri wa amrihim

Shabbahan niʿamatu lā ṭayra wa lā jamal

Qāma bi ṭabʿhā wa nashrihā naẓīmuhā Ahmad al-Tijjānī Tukur

wa Sharīkuhu Abū Bakr Masʿūdu. Wa qāhumā l-Lāhu

Sharran wa ḍayran. Āmin, bi ḥaqqi l-ʿālamīn.

Ṭabʿat al-ūla 1963

Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Human Being Is an Incurable Disease." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/paden-047-mutum-cuta-ne-marar-magani/.

[Page 1]

Bismi l-Lāhi al-Raḥmān al-Raḥīm Wa ṣalla l-Lāhu ʿalā l-Nabiyyil karīm

Jama'a ku saurareni ga wata tambaya Shin wa ya ganemin halinsu mutane

Rannan ina zance da Shaho, sai ya ce Dan Allah yaya ne halinku mutane

Mu dukka tsuntsaye muna daɗa tambaya Mun kasa ganewar halinku mutane

Ni ko na'amsa mai na ce masa ya kake Mani tambayar raini game da mutane

Yai wuf ya ce ai mu dabara ce damu Domin hakannan munka gane mutane

Na ko ce da Shaho, kai haba yaya suke? Ni dai ina fata in gane mutane

Sai kuwa ya ce mani roɗi-roɗi da ja suke Kai har da kore, rawaya da mutane

Balle fa ƴan yau ka ji zo na gaya maka Cutar da ba ta da magani daɗa sune

Har hankali wallahi ka ji yakan ɓace Bisa kan ɗabi'o'insu ka ji mutane

In ka yi kyauta sai su ce mai fariya In ka ruƙe hannunka mai rowa ne

In ka shigesu su ce da kai mai san lasu Kai wane sai kwaɗayin tsiya da mutane

Kuma in ka kame ba ka roƙon ko kobo Ka ƙyale kowa da abinsa ka gane

Maza sai a ce maka wane lallai yai kuɗi Domin hakannan ba shi da ladabi ne

In ko ka ji masu tambayar ko ɗan sule Sun san abin tono wajansu mutane

[Page 2]

"Wai ane yau ya zo in ba shi sule kaza Hauka nake yi? Na hana shi ka gane"

Shaho ya ce min "Ga kaɗan na rattaba" Kai me ka fuskanta game da mutane?

Ai na ce masa "Babu suka ko kaɗan Wannan hali duk na garemu mutane"

Kuma in karatu ne da kai daɗa ka jiya In har ka kame za su ƙi ka mutane

Haka in ka ja su, su ce da kai "Wai malami Mu ba ruwanmu da gargarɗinsa ya gane" Aba

tun da munka yi sai na gane ka jiya! Ba mai gwaninta gunsu ka ji mutane

In kai gajere ne, su ce ɗan ƙanƙani    Mai ɗan tsawo kuma sai su ce dogo ne
In ba ruwanka dasu, su zam maka bincike    Wai kai shaqiyyi ne garesu mutane
In ko ka kwanta gaisuwa gun shugaban    Ka su ce da kai ladabinka duk na kuɗi ne
In ko ka ɗauke kanka babu ruwanka sam,    Daɗa sai su ce maka wallah girman kai ne
Wa zai nufin kuɓuta a filin duniya?    Wallahi yai wahala garesu mutane
Dan ga musali wanda anka aje mana    Luƙumanu ya nuna waɗansu mutane
Shine ya hau jaki fa ɗansa yana ƙasa    Suka ce da shi bai tausayi, ji mutane
Sannan ya sau kafa ɗansa shi ya haye sama    Aka ce da shi san ɗa gareshi, ka gane!
Suka hau gaba ɗaya, nan-da-nan aka ce dasu    Ba tausayi a garesu ko na ɗari ne

[Page 3]

Mai za ka ce da mutum a filin duniya?    Komai abunda ka yo buris da mutane Zan ce
nda munka yi ni da shaihun malami    Ai sai na gane zama da ni da mutane
Babban abinda na tambaya, ƴan uwa,    Dukkan halitta, wa l-Lāh, ba ya mutane
Amma halinsu yana da cuta mai dafi    Balle na yanzu halin zama da mutane
Su malami bai tsira, balle jahili    Kuɗi sha'aninsu, ka ji mutane
Komai sarauta, wa l-Lāh, duk ba su bar shi ba    Ko da maras komai wajensu mutane
Shaho ya ce min "Za na bar ka a nan haka    Sauri nake yi yanzu, ka ji mutane"
Nai godiya a gareshi sai ya ɓace mani    Nai al-ʿajab Shaho da gane mutane
Jamaʿa batu nan, wa l-Lāh, ba a musu nasa    Sai dai ragewa kan halinsu mutane
In banda halin ɗan Adam mai gardama    Ba ya ganin laifinsa sai na mutane
In ka zamo kai mai kawaici ne daɗa,    Ba ka yawan magana ƙwarai da mutane.
Nan take za fa su ce da kai mai son isa    Mai gaida kowa, ko a ce kwaɗayi ne
Su dai mutane sai ka ce jumuna suke    Ita ta fi tsuntsaye kamar ta dabanne

| | |
|---|---|
| Ba ta kai kamar kuma raƙumi ba wajen | Tsayi to kamji rikitarwa ta su ko mutane |
| Ba ka goninta gunsu ko da wa kake | Sha'aninsu ya rikitar da masu tunani |

[Page 4]

| | |
|---|---|
| In ka tsaya sallah su ce mai fariya | Duk ƙoƙarinsa ya tabbata wa mutane |
| In ko ka zauna ba karatu sai su ce | Ai jahili ne, ba karatu wane |
| In ko daɗa kana ƙoƙari bisa kan sani | Su tsaneka wai kai za ka cinye mutane |
| In ka yi ado, ko su ce da kai wai shin ina | Aka san abinda yake faɗansa ne ne |
| Koko su sami abin faɗa su faɗa maka | Wallahi sai haƙuri zama da mutane |
| Mai dariya ko su ce da shi mara hankali | Mai turɓune fuska ko ƙin ladabi ne |
| Mai ƙin ado ko su ce da shi mai mammaƙo | Ɗoye kuɗinsa yake gami da mutane |
| Kanko kana ɗaki zamanka gida kake, | Sai an tsaneka munafuki ga mutane, |
| Baya zuwa suna bare fa jana'iza | In ko yana ta zuwa ka ji su mutane |
| Sun dami zanchen wane ya cika zallaha | Koma yana fata a zam mutuwa ne? |
| Kai ƴan uwa wallahi kadda muna futa | Ku ɓutar mutum da wuya wajensu mutane |
| In za ka zan aikinka kai dai aikata, | Dan Allah kar ka tsaya ganin ta mutane |
| Kai dai ka 'aikata gaskia ko ya take | Ko dai da ta yi wuya ga mutane |
| To ga ka ɗannan na faɗa bisa kan sani | Aikin da za ka yi duniya ga mutane |
| In za ka 'aikata aiyukanka ka 'aikata, | In ko ka barshi kana gudun ta mutane |

[Page 5]

| | |
|---|---|
| Kai sai a barka kawai kana nan sasuƙai | Ka rotsa kanka gudun ta mutane |
| Ɗan gwargwado dai ga shi na jera maka | Dan Allah dosa tunani ga mutane |
| Sannan ka ɗauko wanga waƙa ka 'aje | Na tabbata ko za ka sake mutane |
| Duk wanda munka faɗa ta sai dai su yi daɗi | Halinsu ya fi gaban a ce waƙe ne |

| | |
|---|---|
| Sai dai azan yin wani littafi guda | Sufuli ɗari yai yo kaɗan ga mutane |
| Har Hausa sun yi karin batunsu kan hakan | Ba'a iyawa duniya da mutane |
| To ƴan uwa sai dai mu zan yin hanƙuri | Kumu kyautatawa kanmu kun ji mutane! |
| Ita duniya nan ka ga ba ƙyalle bace | Ka ma yi kirki ya kake da mutane. |
| Balle a ce kuma ga shi ka zama ja'iri, | Mai zangalewa dan ka ƴanta mutane |
| Jama'ah mu ɗau haƙuri mu zauna lafiya, | Kuma kar mu dosa musu ƙwarai da mutane |
| Kuma kar mu sassautawa sha'anin duniya, | Dana lahira dan kar su ƙi mu mutane |
| Kuma kar mu yarda mu zam bajinta dan yabo | Mu dai mu yo ɗan taimako ga mutane |
| Komai ka yo ɗan Adam fa ka tabbata | Allahu zai saka walau kallo ne |
| In dai akwai cuta a kallon ka jiya? | Kai dai ka zauna lafiya da mutane |
| Kuma kar ka bisu akan abinda suke so | In dai abin nan babu kyau fa ka gane! |

[Page 6]

| | |
|---|---|
| Nai ḥamda l-Lāh nan kun ji kam zan dakata | Dan Allah kai tsaidan ka gane mutane |
| Kuma sai ku ɗau haƙuri da hirannan da ni | Shaho da kyau fa to ya gane mutane |
| Balle fa mu da muke gani da idan duna | Ga hankali a garemu sa da tunani |
| Kuma kar ka damu da duk abinda suke faɗa | Dukkan abinda kasa gaba yi ka kanne! |
| Dan Allah na roƙeku kar ku ƙule da ni | Dan gaskiya ce mai wuya ga mutane |
| Halinsu ne wallahi shi muka rattaba | In kai tunani za ka gane mutane |
| Waƙarda munka yi sai ka ce hoto take | In ka karanta za ka gane mutane |
| Ahmad Tukur shi ne yayo waƙarnana | Shi ma mutum ne mai zama da mutane |
| Ƙarshen yabo na nai yabo ga maɗaukaki, | Manzonmu Aḥmadu shugabanmu mutane, |
| Mai kyan-Ṭabīʿa wan-ʿAliyyu da Jaʿfaru | Ran lahira cetonka duk ga mutane |
| Ka saka da mu domin a gafarta mana | Saɓonda munka yi dan zama da mutane |

Mu dai muna ƙaunarka baban Faṭima Dukkan Musulmi Aljanu da mutane

Wa salām a nanne wagga waƙa ta tsaya Bisa kan bayanina da ni da mutane

Tammat Khaṭṭu bi ʿawni l-Lāhi
Wa law Lāhu lam aktubat
Baytan wāhidan